Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.16 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Kwatancin Halayen Masu Nakasar Kisan-Raɓa Tsakanin Al'umma Da 'Yan Taurin Kassu Zurmi

**Ibrahim Dalha**

Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Tsangayar Fasaha, Jami'ar Usmanu Danfodiyo, Sakkwato

**Corresponding Author: Ibrahim Dalha** ibrahimdalha1@gmail.com
Lambar Waya: 08060574254

**Tsakure**

Duk da cewar waƙoƙin Makaɗa Kassu Zurmi sun fi mayar da hankali a kan rukunin maza ('yan tauri); hakan bai hana a iya ƙyllaro hoton wasu mutane a cikinsu ba. Wannan takarda ta dubi rukunin masu fama da nakasar kisan-raɓa a waƙoƙin da Abubakar Kassu Zurmi ya yi wa 'yan taurinsa. Nazarin ya mayar da hankali ga waƙar Shayi ɗan gidan Labbo a matsayin karan bara. Domin yi wa binciken adalci, an waiwayi ayyukan magabata wallafaffu da waɗanda ba a wallafa ba. Wasu daga cikin hanyoyin tattara bayanan da aka yi amfani da su sun haɗa da: Sauraren waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi da gudanar da hira ko tattaunawa da waɗanda suke da masaniya game da nazarin da aka gudanar, sai kuma karance-karance. Maƙalar ta yi amfani da tunanin Bahaushe (karin magana) da ke cewa: "Maƙwabcin mai kanwa ba ya rasa ɗan ɓarɓashi" a matsayin hanyar ɗora aiki. Wasu daga cikin sakamakon da nazarin ya gano sun haɗa da: Nakasar kisan-raɓa ɗaya ce daga cikin larurorin da suke addabar wasu mutane. Har wa yau, kisan–raɓa nakasa ce da ta shafi mutuwar zuciya, don haka ba a ganin ta ƙuru-ƙuru da ido, sai dai ayyukan wanda ta kama su nuna. Bugu da ƙari, Kisan-raɓa nakasa ce da takan riski wasu a dalilin sakaci, wasu kuma ƙaddara ce ta riga fata. Daga cikin shawarwarin da takardar ta gano sun haɗa da, akwai buƙatar al'umma su sanya wa kansu kishin kai, ta yadda kowa zai tashi ya nemi na kansa kamar yadda magabatanmu suka gudanar da rayuwarsu. Haka kuma, sanya yara a tafarkin jin daɗi, wani abu ne da zai ci gaba da haifar da wannan larura. Domin ko ba komai, idan muka tuna magabata, masu larurar makanta da gurgunta duka suna tashi tsaye su yi sana'a domin samar wa kansu mafita.

**Keɓaɓɓun Kalmomi:** Halaye da Kisan-raɓa da kuma 'Yan Tauri

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Shimfiɗa

Waƙoƙin baka na Hausa a wurin manazarta tamkar wasu fitilu ne da suke haska wa al'umma hoton al'adun Hausawa. Hasali ma, mawaƙa kamar wata taska ce ta adana harshe da adabi da kuma al'adun Hausawa. Wannan dalili ya sa idan wata al'ada ta al'umma ta yi ɓatan dabo, waƙoƙin baka na Hausa suna ɗaya daga cikin taskokin da ake leƙawa a lalubo yanayin yadda take da kuma yadda ake gudanar da ita. Don haka mawaƙan baka na Hausa suka zama jagororin kiyaye al'adun Hausawa tare da rayar da su ta hanyar lugude su a cikin waƙoƙinsu. Dalilin haka ya sanya mai neman sanin yanayin siyasar Hausawa idan ya ratsi waƙoƙin fada zai ji shi warkal irin na wanda ya shiga rijiya da dawonsa. Haka abin yake ga mai neman fahimtar jarumtar Hausawa idan ya saurari waƙoƙin maza. Ga wanda yake buƙatar sanin tattalin arzikin Hausawa idan ya saurari waƙoƙin makaɗan sana'a zai tabbata ruwa na ƙasa sai ga wanda bai tona ba. Mai laluben yanayin nishaɗi da walwalar Hausawa kuwa idan ya ci karo da mawaƙan ban-dariya kayansa ya tsinke a gindin kaba. Wannan magana ta dace da ra'ayin Gusau, (2003:23) inda ya nuna cewa, "waƙoƙin baka na Hausa suna nan jibge kuma sun ratsa dukkanin sassan rayuwa ta fuskar zamantakewa da siyasar zama ko tattalin arziki ko addini ko ta hayar al'adu ko wasanni da sauransu."

Muradin wannan takarda ne ta dubi rukunin wasu nakasassu da aka yi wa laƙabi da masu kisan-raɓa a tsakanin al'umma da 'yan taurin da Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya waƙe. Duk da kasancewar waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi sun fi mayar da hankali a kan rukunin maza ('yan tauri). Wannan bai hana a iya ƙyllaro hoton wasu mutane a cikinsu ba. Don haka aka himmatu a kan bayyana wasu daga cikin ɗabi'u da yanayin masu fama da nakasar kisan-raɓa a wasu daga cikin ɗiyan waƙoƙinsa.

### 1.1 Bayanin Muhimman Kalmomin Taken Takarda

A wannan muhalli an waiwayi ma'anonin muhimman kalmomin da aka gina taken takardar da su, domin fayyace inda bayanan da nazarin ya ƙunsa cikin sauƙi. Kalmomin da aka bayyana ma'anoninsu sun haɗa da: Halaye da da kisan-raɓa da kuma 'yan tauri.

#### 1.1.1 Halaye

CNHN, (2006:191) an bayyana kalmar hali da, "ɗabi'a musamman ta mutum." Wannan takarda, ta lura da cewa, kalmar hali tilo ce, jam'inta shi ne halaye. Ma'anar da ƙamusi ya bayyana ta dace da manufar wannan takarda.

#### 1.1.2 Kisan-raɓa

Duk da cewa, CNHN, (2006:247) an bayyana ma'anar kalmar kisan-raɓa da, "tsumburarriyar tunkiya ko akuya." Akwai buƙatar a fahimta cewa, kiran masu larurar mutuwar zuciya da sunan kisan-raɓa suna ne na fannu wanda nakasassu (masu buƙata ta musamman) suke amfani da shi. Don haka ba kowane gama-garin Bahaushe ne ya san rukunin mutanen da zuciyarsu ta mutu da wannan suna ba. Wannan dalili ya sa aka samu takin-saƙa tsakanin ma'anar da wannan takartda ta bayar da wadda *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero* ya bayyana. Kenan , a fahimtar wannan takarda, kalmar kisan-raɓa ita ce:

> "Wata larura ce da take samun mutum ko kuma lalacinsa ya janyo masa ita. Larurar takan kashe zuciyar mai ɗauke da ita ta yadda ba zai iya taɓuka komai kamar yadda kowane mutum

> yake gudanarwa ba. Idan ta shiga jikin mutum yakan gaza son duk wani aiki na wahala, duk kuwa da ƙoshin lafiyar da yake da ita (saboda ba makaho ko kuturu ko kuma gurgu ba ne). Babu abin da yake gabansa daga kwanciya sai bacci (kwana). Duk da cewa, mai larurar idan ya ga haza yakan tashi ya yi bara ko maula ko kuma tumasanci, domin ya samu abin da zai kai bakinsa.

Da alama, yanayin masu larurar na kasancewarsu kowane lokaci kwance a inuwa mai sanyi da rashin son shiga rana domin neman na kai, shi ne ya janyo aka ambace su da wannan suna. Sakamakon idan aka bi taliyon kalmar a farfajiyar nazarin harshe, kalmomi biyu aka haɗa suka samar da ita, wato, kisa da kuma raɓa. Wannan dalilin ya sanya ake rubuta kalmar ta hanyar amfani da karan ɗori, wato harɗantawa a wurin masana ilimin ƙirar kalma.

**1.1.3 'Yan Tauri**

Bunza, (2006:51) da Darma, (2014:33) sun haƙiƙance da cewa, "asalin tauri daga farauta ne ake shahara a zama ɗan tauri." Ga al'ada, Hausawa sukan yi wa mutum laƙabi daidai da wata halayyarsa ko kuma ɗabi'arsa. Idan an lura, kalmar tauri Hausawa suna bayyana ta ga mutumin da ya yi amfani da wani magani wanda a dalilinsa, makami (ƙarfe ko tsini) ba sa yanka ko huda jikinsa. Hakan ya sa CNHN, (2006:433) aka bayyana tauri da, "maganin da ake ci don kashe kaifin wuƙa ko wani makami don ya kasa huda jikin mutum." Shi kuwa Magaji, (2016:4) ya bayyana kalmar tauri da, "wani abu da ba ya huduwa ko ba ya yankuwa. Wato abin nufi shi ne, wasu magunguna da Hausawa suke amfani da su domin kare kansu daga yanka ko sara ko kuma hudawa na duk wani makami mai kaiffi ko mai tsini, musamman na ƙarfe. Ainihin sunan abin shi ne maganin sanya taurin jiki, wanda har ya komo ana kiran sa tauri kawai." Kenan, wannan ma'ana ta nuna cewa, 'yan tauri su ne nau'in mutanen da sukan yi amfani da maganin kashe kaifi ko tsinin wuƙa ko kuma wani makami ta yadda ba zai iya yankawa ko kuma huda jikinsu ba. Shi ne ya sa Makaɗa Kassu Zurmi yake cewa:

Jagora: Tauri wuya garai sai a yi ƙoƙari,
: A sha malamai a ɗebi sayyu a yi kariya.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shehu Guraguri).

**2.0 Hanyoyin Bincike**

Masu magana ba su yi laifi ba da suke cewa: "A rashin kira karen Bebe ya ɓata." Hakan bai rasa nasaba da fahimtar da suka yi dangane da lamarin duniya, inda sukan ce sanin wurin bugu shi ne ƙira. Domin suna da yaƙinin cewa, idan raƙuminka ya ɓata har ramin ɓera kana da damar ka rega. Wannan dalili ya sanya wannan takarda ta yi amfani da wasu hanyoyin tattaro bayanai waɗanda suka haɗa da:

i. An yi ƙoƙarin sauraren waƙoƙin Abubakar Kassu Zurmi a na'urar adana bayanai ta memori da ake sanya wa a wayar hannu.
ii. An karanci littafin *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa* wanda Magaji (2016) ya wallafa. Karanta wannan littafi ya ƙara wa wannan takarda haske musamman wajen fahimtar lafuzan kalmomin da Makaɗa Kassu Zurmi yake amfani da su a waƙoƙinsa. Bugu da ƙari, karanta wannan littafi ya cike wa wannan takarda giɓin da ta samu a tsakanin abin da yake rubuce da kuma wanda ya rera da bakinsa.

iii. Har wa yau, an yi ƙoƙarin dubin wasu daga cikin ayyukan da aka nazarci al'ada a cikin adabi, domin sanin inda aka tunkara. A wannan hauji ne aka yi ƙoƙarin yin ido biyu da wasu daga cikin ayyukan al'ada da aka gudanar da su ta hayar amfani da wasu sassan adabi. Misali, Kabakawa, (2012) da Ayuba, (2013) da kuma Sanyinnawal (2015) da sauransu.

iv. Takardar ba ta yi ƙasa a guiwa ba wajen tuntuɓar wasu masana al'ada da kuma mutanen da suke da masaniya game da waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi, inda aka yi musu tambayoyi a kan batun da ake tattaunawa.

v. Haka kuma, wannan takarda ta amfana da shafin *WhatsApp* da aka buɗe saboda yayata wannan taro, inda masana da manazarta suka yi ta tattauna muhimman bayanai game da rayuwa da kuma waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi.

vi. A wani hanzari ba gudu ba, an amfana da sauraren hirar da aka yi da Alhaji Ibrahim Muhammad (Maigirma Ɗanmadamin Birnin Magaji) a kan rayuwa da waƙoƙin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi. An gudanar da wannan hira a Rediyon Nijeriya na Kaduna (FRCN) a shekarar 2019.

## 2.1 Hanyar Ɗora Aiki

Idan aka dubi bayanan da Bunza (2019) da Bala (2021) da Sani (2022) da kuma Ɗalha (2024) suka bayar dangane ƙunshiyar ma'anar hanyar ɗora aiki. Sun ƙara tabbatar da cewa, wata maɓuɓɓuga ce ta ilimi wadda wasu magabata suka samar domin yin jagora ga ayyukan bincike. Hakan ya sa wannan takarda ta yi amfani da tunanin Hausawa domin ɗora nazarin a kansa. Domin ko ba komai, nazari ne da aka gudanar da shi a kan wani rukuni na Hausawa. Don haka akwai buƙatar a yi amfani da tunaninsu domin gudanar da shi, saboda gaskata maganar Hausawa da take cewa: "Karen duk da ya yi cizo da gashinsa ake magani. Sakamakon haka, an ɗora wannan takarda a kan tunanin Hausawa da yake cewa: "Maƙwabcin mai kanwa ba ya rasa ɗan ɓarɓashi. "
An yi amfani da wannan tunani ne saboda hango alaƙar da take tsakanin mai nakasar sassan jiki da ake iya gani da kuma wanda yake fama da larurar mutuwar zuciya wadda ido ba ya gani sai dai a gan ta a aikace. Kenan, kusancin mai nakasar kisan-raɓa da masu nakasar sassan jiki na makanta da kuturta da gurguntaka yana da alaƙa da na masu mutuwar zuciya. Don haka suka zama maƙwabtan juna, saboda da abokin daka akan sha gari.

## 3.0 Da Walakin Goro a Cikin Miya

A wurin masana lamarin tauri, akwai wani nau'in maganin tauri da akan yi amfani da shi wanda ake kira da baƙin tauri ko kuma "kicik[1]." Wannan nau'i na tauri, masu amfani da shi sukan zama na daban a cikin 'yan tauri. Dalili kuwa, sukan kasance ba sa neman arziki, kamar yadda arzikin kansa ba ya nemansu[2]. Hasali ma masu tu'ammali da wannan nau'in tauri ko nagartaccen tufafi ba sa sanyawa. Magaji, (2016:6) ya bayyana cewa, "ko tufa ba ta daɗewa a jikinsu sai ta kekkece." Galiban duk abin da suke ganin idan sun aikata za su samu wani arziki ba sa gudanar da shi. Sun fi sha'awar su zauna ba tare da komai ba, sai dai kawai su shagala da wannan harkar tauri da suka sanya a gaba. Da alama yanayin ɗabi'un waɗannan rukuni na 'yan tauri shi ne ya ja hankalin wannan takarda inda

[1] Hira da Malam Buhari Lawali na Kwalejin Ilimi ta Shehu Shagari, Sakkwato ranar 21/04/2025 ta wayar hannu.
[2] Farfesa Yakubu Aliyu Gobir na Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, Sakkwato ya ba da labarin wani ɗan tauri da wani Sarki ya ce da shi ya ɗauko igiya (tsawo) a ɗaura masa kyautar damen hatsi. Rashin yarda (ƙuiwa) ya nemo igiya shi ya hana masa wannan kyauta. Tare da cewa, igiyar ba ta yi wahalar samu ba. Wannan yana daga cikin halayyar masu wannan nau'i na tauri.

ta kwatanta su da al'ummar da suke da nakasar kisan-raɓa (mutuwar zuciya). Duk da cewa, su ('yan taurin) ba nakasa ce a gare su ba; yanayin taurin da suke tu'ammali da shi ne yake mayar da su cikin irin wannan ɗabi'a. Shayi ɗan Gidan Labbo da Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya yi wa waƙa yana daga cikin rukunin waɗannan 'yan tauri da suka yi amfani da salon tauri na kicik (baƙin tauri). Bayanin da makaɗa ya yi a kansa shi ya tabbatar da haka.

### 3.1 Kisan-raɓa a Farfajiyar Nazari

Kusan ana iya cewa, da yawa daga cikin mutane idan aka ambaci mutanen da suke da larura sun fi karkata a kan waɗanda suka samu nakasa ta fuskar gani (makafi) da kutare da guragu da kuma kurame. An manta da cewa, akwai mutanen da suke da ƙoshin lafiya ta fuskar larurorin da aka ambata a baya, amma hakan bai sanya sun shiga cikin mutane lafiyayyu ba. Hakan bai rasa nasaba da yanayin da suka sanya kansu ko kuma suka tsinci kansu na rayuwa.

Ga al'ada, ba kowane lokaci masu larurar kisan-raɓa suke sanya sababbin tufafi ba. Sakamakon a kowane lokaci suna son su nuna wa mutane suna neman agajinsu ne. Sukan sanya tufafin cikin tsarin yanayin riga ta sha bamban da wando. Wani lokaci ma, idan aka ga sun sauya tufafi aro shi suka yi daga wurin 'yan'uwa da abokan arziki. Irin wannan halayya ce Makaɗa yake yi wa al'umma kwatance da abin da ya faru da tauraronsa Shayi ɗan gidan Labbo, kamar yadda yake cewa:

Jagora : Wasan da munka zo tare da 'yan Magarya tai kyawo,
: Rannan Sha-yaya yas shigo sa'a,
: Ga ya da dogon baki da yaw wutab ɓota,
: Na Abu yankan bakinka ya yi ma kyawo,
: **Ya samu gama aron zanen saƙi,**
**: Had da tsamiya yaɗ ɗauro da yab baƙas shadda.**
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan Gidan Labbo).

Duk da cewa, yanayin maganin taurin da 'yan tauri sukan sha yana hana musu sanya tufafi. Sakamakon zafin da taurin yake da shi, saboda haka ma wasunsu sukan ƙare rayuwarsu cikin warki (walki)[3]. 'Yan tauri suna amfani da warki ne saboda tufafi ba zai daɗe a jikinsu ba. Wannan ya sanya sukan zama tamkar masu nakasar kisan-raɓa, musamman idan aka dubi yadda ba sa wani ado ko sanya tufafi mai kyau.

Dangane da yanayin ire-iren masu kisan-raɓa kuwa, wannan takarda tana da ra'ayin raba su zuwa ɓangarori guda biyu kamar haka:

i. Masu gudanar da bara
ii. Waɗanda ba sa bara

### 3.2 Masu Gudanar da Bara

Ga waɗanda suke gudanar da bara, mafiya yawancinsu suna shiga cikin rukunin makafi ne. Don haka Hambali(2025)[4] ya tabbatar wa da wannan takarda cewa, suna ƙarƙashin ikon Sarkin Makafi ne. Don haka suka fi gudanar da ma'amalar bara tare da su. Da alama yanayin nakasar kuturta ta shiga cikin rukunin cutukan da ake ɗauka, shi ne ya sanya masu nakasar kisan-raɓa ba sa shiga cikin kutare. Su kuwa guragu yanayin ɗabi'unsu na ƙiriniya shi ne ya sanya tasu ba ta cika zama daidai da masu larurar kisan-

[3] Warki/walki dai gajeriyar fata ce jemammiya yawanci baƙa wadda ake ɗaurawa a gindi ko a yafa (CNHN, 2006:469).
[4] Hira da Sarkin Makafi Hambali, wani Sarkin Makafi da yake zaune a jihar Jigawa, ranar 25/02/2025.

raɓa ba. Yanayin mu'amala da kurame dole yana buƙatar ƙwarewa wajen magana da su, hakan shi yake yi wa masu larurar kisan-raɓa tarnaƙi na yin hulɗa da su.

Dangane da yanayin gudanar da bara a wurin masu larurar kisan-raɓa kuwa, da wahala ka riske su suna gudanar da barar ta hanyar rera waƙe kamar yadda sauran mabarata sukan yi. Galiban sukan gudanar da bara ba tare da wani waƙe ba. Suna dai cewa: "A ba ni/mu saboda Allah da Manzonsa." Wani lokaci kuma sukan riƙa faɗin, "Fi Sabilillah!" Sukan tsaya a wurin taruwar jama'a kamar Masallaci da sauran wurare, tare da bayyana musu daumuwarsu ta rashin abinci da dangoginta, saboda a agaza musu. Mata kuma sun fi shiga gidaje suna bara. Kodayake wani lokaci sukan tsaya a gefen hanya ko wuraren taruwar jama'a. Wasu daga cikin mata sukan goyi yaro ko yarinya inda sukan sanya musu kaya marasa kyau domin hakan ya ja hankalin mai bayar da sadaka ya agaza musu. Hasali ma wasu daga cikinsu sukan yi garkuwa da yanayin rashin tsaro da ƙasarmu take fama da shi wajen neman taimako. Duk kuwa da cewa, ba duka aka taru aka zama ɗaya ba.

### 3.3 Waɗanda Ba Sa Bara

A fage guda kuma, akwai wasu nau'in masu kisan-raɓa waɗanda ba sa bara, sai dai su ɗora takalifin rayuwarsu a kan makusantansu (yayyu da ƙanne/iyaye) da kuma sauran 'yan'uwa da abokan arziki. Irin waɗannan mutane suna ɗaukar bara a matsayin ƙasƙanci duk da cewa, zuciyarsu ta mutu, saboda haka ba sa iya gudanar da wata sana'a a matsayin abin dogaro a gare su. Masu irin wannan larura babu abin da yake gabansu a kowane lokaci sai yawan bacci (kwana). Hasali ma, shi ne dalilin da ya sa riƙon iyali yake gagararsu. Sakamakon haka, iyalan da suke ƙarƙashinsu su ne suke ɗaukar takalifin rayuwarsu. Makaɗa ya yi mana nuni da wannan yanayi nasu ta hanyar fito da hoton abin ga Shayi ɗan Gidan Labbo (duk da cewa, shi ba kisan-raɓa ba ne) inda yake cewa:

Jagora : Ni ce, I gaskiyakka dattijo,
: Mutum kau ba za ya kai ɗiya tai ba,
: Gidan da ba abin kirki,
: Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi,
: Sai ɗiyad dattijai kaɗai ka amren,
: Sha-yaya ɗan gidan Labbo, na Abu,
: **Tunda kowa amre shi ita ka cishe shi,**
**: Ta biya kuɗin garin karen kyasko,**
**: Sannan ta yi mai abin ruhwa,**
**: Kana ta koma ta yi dabdalin abin ɗamri.**
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan Gidan Labbo).

Ɗabi'ar 'Yan tauri ta shagala da abubuwan da suke gabansu na farauta da shan magungunan kariya saboda abokan gaba, shi ne ya sanya ba kowane lokaci suke sauraren iyalansu ba ballantana su san halin da suke ciki. Hasali ma wani lokaci sukan ɗauki lokaci mai tsawo suna cikin daji. Hakan ya sa dole iyalansu su riƙa ɗaukar takalihun rayuwarsu ta wasu ɓangarori. Wannan ɗabi'a, takan sanya su yi kama da masu nakasar kisan-raɓa.

### 3.4 Matsalolin da Suke Haifar da Nakasar Kisan-raɓa

Ga al'ada, ruwa ba ya tsami banza, saboda haka Hausawa suke cewa: "Idan ka ji gudu da labari." Kowane abu yana da musabbabin faruwarsa. Kamar yadda larurar makanta takan auku a dalilin lalacewar idanu. Gurguntaka kuma takan samu ga jikin ɗan'adam saboda lalacewar wata gaɓa. Haka lamarin yake ga masu cutar kuturta da kurumta. Wannan ya nuna cewa, ita ma larurar kisan-raɓa tana da wasu matsaloli da suke

haifar da ita. Wasu daga cikin matsalolin da wannan takarda ta kai ga hangowa sun haɗa da:

### 3.4.1 Gata (shagwaɓa)

Gata a wannan muhallai ana nufin ɗaukar takalifin mutum mai lafiyayyen hankali da sassan jiki, tare da hana masa yin wani takaɓus da zai taimake shi walau na neman ilimi ko kuma na sana'a. Da yawa daga cikin waɗanda suka kamu da wannan larura ba a nuna musu tashi a nemi na kai yana da alfanu, saboda haka suka shantake har abin ya zame musu larura. A wani lokaci buƙatunsu na rayuwa sukan taso, maimakon a tarbiyantar da su ga yadda ake tattali da tsari har a kai ga cimma biyan buƙata, sai a karɓe musu. Makaɗa ya ba mu kwatancin wannan halayya lokacin da yake bayyana abin da ya faru ga Shayi ɗan Gidan Labbo yayin da buƙatar aure ta taso masa, don haka Makaɗa Kassu yake cewa:

Jagora : Don an game da Labbo yana tattalin ɗiyan dangi,
: To daɗa ra amren Sha, Labbo ya wahala,
: Ra amren sha, Labbo yai yawo,
: Yai yawo,
: Amren Sha-yaya Labbo ya yi jidali.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

### 3.4.2 Zama Wuri Guda da Nakasassu

Al'adar ɗan'adam idan ya zauna wuri guda da wani mutum mai wata ɗabi'a, yakan tsinci wani abu daga cikin halayensa kamar yadda shi wancan abokin zaman nasa zai ɗauka daga gare shi. Wannan dalili ya sa masu hikima suke cewa: "Zama wuri guda da wuta, shi ya sanya ruwa ya ɗauki ɗabi'ar ƙona mutum, ba domin halinsa ba ne." Zama tare da naƙasassu yakan sanya mai matacciyar zuciya ya kasa taɓuka komai sai tunanin yadda zai yi ya samu ba tare da ya sha wahala ba. Hasali ma, wasu masu larurar kisan-raɓa sun tasirantu da ɗabi'ar bara ne saboda ayyukan jagorancin makafi da suka yi. Sakamakon a manyan birane, yi wa makafi jagora wata sana'a ce da wasu sukan fita ci-rani domin gudanar da ita. Kamar yadda masu larurar makanta da gurguntaka da kuturta sukan zauna sai abin da aka rage aka ba su, haka su ma masu nakasar kisan-raɓa sukan yi. Makaɗa ya ɗauko hoton wannan halayya inda ya yi garkuwa da Shayi domin ya kwatanta wa al'umma. Ga abin da yake cewa:

Jagora : Ta Ɗangiwa Hauwa na yi mai biɗa,
: Ba ta da ƙarhi ba ta biyak kuyya,
: Yat tahwasa taka ɗiba a ba ta sadare,
: Ta kau ci hat ta cishe shi,
: Taro kun san ko Hauwa ubanai ce.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

### 3.4.3 Mutuwar Zuciya

Cuɗanyar Hausawa da wasu ƙabilu da kuma kankamar mulkin siyasa ya dagula wa wasu daga cikinsu tunani. A baya, kowane gidan Bahaushe yana da wata sana'ada da ya dogara da ita. Abin ya kai ga wasu zuriyoyin Hausawa ma ana kallon su da sana'oin da suka gada kaka da kakanni. Sannu a hankali, sai al'umma masu tasowa suka fara sauya wannan kyakkyawan tarihi na Hausawa, inda suka ɗauki ɗabi'un tumasanci da maula suka yafa. Abin ya kai ga matasa lafiyayyu sukan laɓe da siyasa su riƙa cin mutuncin waɗanda suka ƙi ba su maula. Wannan matsala ta kai mutane da dama faɗawa cikin masu

nakasar kisan-raɓa. Lamarin ya yi ƙamarin da Makaɗa yake kwatanta hoton wannan nakasa a cikin waƙar Shayi ɗan Gidan Labbo domin ya haska wa al'umma ita, inda yake cewa:

Jagora : Katakoron Lando, Iro na Ummaru,
: Kura mai guzurin kunya,
: Sha-yaya Magarya ta yi ma doro,
: Tana nan ta bar ka, Alu ta tcere,
: Dauri an bar maka tsohuwa ta cishe ka,
: Tsohuwag ga ta tuzge,
: To daɗa Sha wa ka cishe ka?
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Mutuwar zuciya ta yi munin da dabba ce take yi wa mai ita nasiha, saboda ya kasa tashi ya nema a lokacin da kowa yake fafutika. Haƙiƙa ko ba a faɗi ba, ga mai zurfin tunani ya san akwai larura a cikin wannan yanayi. Dubi abin da Makaɗa Kassu yake faɗi a nan:

Jagora : Kakab bana tai kyawo,
: Ko ta bara mun gode,
: Sai dai Sha-yaya bai yi komai ba,
: Na ga 'yan tantabaru cikin ruhewarsu,
: Tantabara goma,
: Amma yanzu ba su sun ƙare,
: Yanzu kam saura nai guda baƙi namiji,
: Ko shi kam dan yana yi mai waƙa,
: Inda sahiya taw waye ya ɗora mabanci.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

### 3.4.5 Raina Sana'a

A tsarin falsafar rayuwa, kowane ɗan'adam yana miƙa ne daidai da mayafinsa. Domin wurin da wani ya yi rawa aka ba shi kuɗi, idan wani ya yi duka zai sha. Don haka Makaɗa Musa Ɗanƙwairo Maradun yake cewa:

Jagora : Inda Allah bai kai mutum ba yac ce ya kai da ƙarhi,
Yara : To ya zam taɓaɓɓe.
Gindi : Jikan Moyi,
: Iro ɗan Mamman tura haushi.
(Musa Ɗanƙwairo: Waƙar Sarkin Maradun).

Wasu mutane suna ɗaukar sana'o'in da suka gada a matsayin ƙasƙantattu, saboda haka sukan gaza tsayawa tsayin daka su koye su kuma su ci moriyarsu. Raina sana'a, shi ya janyo Makaɗa yake yi wa al'umma bayanin illar da ke cikin wannan ɗabi'a. Makaɗa ya laɓe da Shayi ɗan Gidan Labbo inda yake nuna yadda ya kasa tsayawa ya yi noma, har ya zama cima-zaune mahaifiyarsa ce take ciyar da shi da tafasar da take nemowa tana sayarwa. Wannan wani kwatance ne da Makaɗa Kassu Zurmi ya yi wa mutane, kasancewarsa makaɗin 'yan tauri, sai ya laɓe da wani daga cikin taurarinsa domin ya ja hankalin mutane a kai. Don haka yake cewa:

Jagora : Kakab bana tai kyawo,
: Ko ta bara mun gode,
: Sai dai Sha-yaya bai yi komai ba,
: ..........................................................
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

**4.0 Ɗabi'un Masu Nakasar Kisan-raɓa**

Kowane ɗan'adam ba ya rasa wata ɗabi'a da ya keɓanta da ita. Wannan ya sa idan al'umma sun haɗu cikin rukuni guda masana al'ada sukan yi musu kallon mutanen da suke da wata keɓantaccoiyar ɗabi'a. Misali, a fannin nakasassu, ana kallon makafi suna da ɗabi'ar jayayya da son bayar da labari da kuma rashin kunya (saboda kunya a ido take). Su kuma Kutare suna da halayyar fushi, yayin da su kuma kurame suke da ɗabi'ar gulma da rashin yafiya (don haka idan aka yi faɗa da su yakan daɗe bai wuce ba).

Dangane da ɗaib'un masu larurar kisan-raɓa kuwa, gwargwadon bayanan da wannan takarda ta kalato suna da waɗannan ɗabi'u:

**4.1 Lalaci**

Lalaci shi ne gaza gudanar da aikin da ake da damar aiwatarwa. Ɗabi'ar lalaci ba ta da mafaka a farfajiyar al'adun Hausawa, saboda idan aka dubi azancin magabatanmu ba su yarda da zaman banza ba. Idan aka dubi waɗannan karin maganganu za su tabbatar da ha:

- Da zaman banza gwara aikin kishiya.
- Da ciwon zuciya, gwara na jiki.
- Zama kurum ɓarna ne.
- Duniya ba ta rago ba ce. Ga su nan dai.

A duk inda masu larurar kisan-raɓa suke za a tarar da su mutuwar da zuciyarsu ta yi ya haifar musu da lalaci wada shi ne yake zama jagoran gaza taɓuka duk wani aiki da zai haifar wa ɗan'adam wata moriya. Kowane lokaci daga kwanciya sai barci (kwana) su ne manyan ayyukansu. Don haka koda lokacin noma ne ba sa iya aikata komai, kamar yadda Makaɗa ya ba da labarin yanayin ɗabi'arsu inda ya yi garkuwa da Shayi ɗan gidan Labbo domin fito da yanayinta.

Jagora : Irin gidan Bawa Ɗangaladima,
: Sai da Bawa yab ba shi sai Taɗari taƙ ƙwace,
: Tac ce sabilin Sha-yaya ba a bashe su,
: Ɗan nema bai raga wa kowa ba,
: Wata 'yar gona garai cikin tabki,
: Bara yat tashi yana kashin awakinmu,
: Tac ce masalin mai ƙato gudun awa Shayi,
: An nan ka biɗab bashi.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

**4.2 Karya**

Karya shi ne aikata wani abu wanda ba a kan gaskiya aka gina shi ba. Yana daga cikin ɗabi'un masu wannan larura, son birge mutane musamman mata. Ga al'ada, mai son birge mata bai fiye cin nasara ba idan bai haɗa da ƙarya ba. Wannan ya sanya a kowane lokaci yake ƙoƙarin sanya tufafin da zai burge su ko da kuwa zai aro su ne daga wurin wani. Dubi hoton abin da Makaɗa yake faɗa a kan wata tafiya da ya yi da Shayi ɗan gidan Labbo. Makaɗa ya ba da wannan labari ne domin ya nuna wa mutane irin ɗabi'unsu, saboda haka ya fake da Shayi ɗan Gidan Labbo saboda ya zama karan-bara.

Jagora : Wasan da munka zo tare da 'yan Magarya,
: Tai kyawo,
: Rannan Sha-yaya yas shigo sa'a,
: Ga ya da dogon baki da yaw wutaɓ ɓota,
: Na Abu yankan bakinka ya yi ma kyawo,

: Ya samu gama aron zanen saƙi,
: Had da tsamiya yaɗ ɗauro da yab baƙas shadda.

Rashin sanin da 'yan mata suka yi cewa, Shayi ɗan gidan Labbo aro kayan da yake jikinsa ya yi, duk kuwa da cewa, makaɗa ya nuna suturar da ya sanya ta ƙayatar da shi, shi ne mata suka kama wasoson ƙaunarsa, kamar yadda yake faɗa:

Jagora : 'Yanmata sun gane shi sun je mai,
: Anka ɗora wasoso,
: Ni wanin Shayi ni ka jiɗe shi,
: A'a kina ƙarya na riga ki zaɓo shi,
: Kamas su buga ga su nan cikin gebe,
: Na ce kak ku buga ya ishe ku jiɗawa.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

**4.3 Son jin daɗi (Holewa)**

Ga lama, lalaci da son ƙarya duka suna faruwa ne ga mutumin da yake da ɗabi'ar son jin daɗi. Sakamakon duk wanda zai tashi ya nemi na kansa dole son jin daɗi ya ragu a wurinsa. Domin wani lokaci ma zai iya hana idonsa barci saboda ya samar wa kansa mafita. Masu larurar kisan-raɓa a kowane lokaci babu abin da ke ransu face holewa da son jin daɗi. Wannan dalili ya sa ba sa iya tashi tsaye su nemi na kansu kamar yadda kowa yakan yi. Don haka a kullum burinsu shi ne gudanar da rayuwa ta jin daɗi ko da kuwa ba su da hali. Kassu ya ba mu kwatancin wannan ɗabi'a, inda ya yi garkuwa da Shayi ɗan gidan Labbo da irin daular da suka sha. Duk kuwa da cewa a cikin waƙar ya nuna tsohuwarsa ce take ciyar da shi saboda mutuwar zuciya. Ga abin da yake cewa:

Jagora : Ɗaukash Sha-yaya munka sha daula,
: Mun sha ɗamnalutsa mun sha mai,
: Mun sha zabbi ga ɗan gidan Labbo,
: Nic ce ma 'yan yarana, ku sha ahaha ce,
: Tunda ba ya maishe ta.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

Son holewa ne yake sanya mutum ya kwanta ya yi ta bacci ba tare da la'akari da lokacin tashi a tafi nema ba. Don haka Makaɗa yake cewa:

Jagora : Tantabari na riganka tasowa,
: Kai ka ga da ranak kwana sai luhwa ta shuɗe,
: Sai tsuntsu ya hito yana shan hantci,
: Yana gashin ƙeya,
: Shina dubin inda za ka hudowa,
: Shi kau yana cikin ɗaki,
: Tantabari na gyaran juki nai.
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi ɗan gidan Labbo).

**4.4 Hanyoyin Magance Larurar Kisan-raɓa**

Gaskiyar Hausawa da suka ce: "Riga-kafi ya fi magani." Sau da yawa, akan hangi matsala, amma rashin samar da maganinta tun daga tushe, yakan sa a kasa shawo kanta. Don haka gano tushen matsala yake zama tamkar wani ɓangare na samun hanyar magance ta. Wannan nazari yana da ra'ayin idan aka tsira wa waɗannan abubuwa ido ƙwarai, sannan kuma aka aiwatar da su a aikace za a samu sauƙin wannan matsala da take yi wa mutane masu tasowa barazana. Hanyoyin kuwa su ne kamar haka:

i. Dawo da tarbiyar al'ummarmu irin yadda magabata suka yi a baya. Hakan zai sanya kowane yaro dole ya koyi sana'ar gidansu koda kuwa zai iya wasu sana'o'i daga baya.
ii. Ilmantar da al'umma tun daga matakin ƙuruciya har zuwa girma.
iii. Taimaka wa masu ƙananan sana'o'i ta fuskoki daban-daban. Gwamnati ta taimake su da jari, su kuma al'umma su riƙa sayen abin da suke samarwa.
iv. Rage dogaro da gwamnati kamar yadda magabatanmu suka yi a baya.
v. "Yan siyasarmu su fara tunanin kafa matasa ta fuskar abin yi maimakon ba su kuɗaɗe barkatai.

### 5.0 Sakamakon Bincike

Daga cikin abubuwan da wannan takarda ta kai ganowa akwai:
i. Nakasar kisan-raɓa ɗaya ce daga cikin larurorin da suke addabar wasu mutane.
ii. Kisan–raɓa nakasa ce da ta shafi mutuwar zuciya, don haka ba a gane ta ƙuru-ƙuru da ido, sai dai ayyukan wanda ta kama su nuna.
iii. Kisan-raɓa nakasa ce da takan riski wasu a dalilin sakaci, wasu kuma ƙaddara ce ta riga fata.
iv. Masu nakasar kisan raɓa suna raɓe da masu larurar makanta don haka, suka zama a ƙarƙashin ikonsu a wuraren da suke bara. Hasali ma, cuɗanyar su da makafi da yi musu ayyukan jagora ya haifar wa da musu ita wannan larurar.
v. Masu larurar suna da rabe-rabe da kuma ɗabi'u. Haka kuma, an kai ga gano dalilan da suke haifar da ita, tare da hanyoyin magance ta.

### 5.1 Shawarwari

Gaskiyar Hausawa da suka ce, mai shawara aikinsa ba ya ɓaci. Wannan takarda tana hasashen idan aka yi amfani da waɗannan shawarwari, za a yi wa wannan larura ƙofar rago.
i. Akwai buƙatar al'umma su sanya wa kansu kishin kai, ta yadda kowa zai tashi ya nemi na kansa kamar yadda magabatanmu suka gudanar da rayuwarsu.
ii. Sanya yara a tafarkin jin daɗi, wani abu ne da zai ci gaba da haifar da wannan larura. Domin ko ba komai, idan muka tuna magabata, masu larurar makanta da gurgunta duka suna tashi tsaye su yi sana'a domin samar wa kansu mafuta.
iii. Yana da kyau shugabanninmu na siyasa, su fara karkatar da kyaututtukan da suke ba matasa, zuwa gina musu wuraren koyan sana'o'in dogaro da kai. Hakan zai sanya su tsira da sana'ar yi, maimakon yau suna nan gobe suna can yawon tumasanci da maula.

### 5.2 Naɗewa

Daga ƙarshe, wannan takarda tamkar tunasarwa ce ga magabatanmu dangane da wannan larura da take nema ta zama ruwan dare a cikin al'ummarmu. Haƙiƙa, Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya haska wa masana da manazarta cewa, matsalar mutuwar zuciya tana iya haddasa komai na lalaci. Duk da cewa, taurararon da ya yi amfani da shi wajen haska wa al'umma wannan nau'in nakasa ba nakasasshe ba ne. Hasali ma ƙasaitaccen jarumin ɗan tauri ne. Makaɗa dai ya yi amfani da hikimarsa ne domin ya nuna wa mutane illar da take tattare da wannan nakasa ta kisan-raɓa (mutuwar zuciya). Koƙarinsa na son mutane su gane saƙonsa shi ne ya sanya ya yi amfani da ɗaya daga cikin taurarinsa (Shayi ɗan Gidan Labbo). Don haka ya bayyana yanayin masu ɗauke da ita domin a fahimci yadda za a daƙile ta. Takardar ta kai ga raba larurar kisan-raɓa zuwa ɓangarori guda biyu, masu gudanar da bara da waɗanda ba sa bara. An fahimci gata

(shagwaɓa) da zama wuri guda da nakasassu da son jin daɗi su ne musabbabin kamuwa da wannan larura. Haka kuma Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya nuna wa mutane cewa, lalaci da ƙarya da son jin daɗi su ne ɗabi'un masu fama da larurar kisan-raɓa, kamar yadda ya bayyana hotonsu a cikin waƙar Shayi ɗan gidan Labbo. Wannan ya tabbatar da cewa, mawaƙanmu na baka sun yi amfani da hikimominsu domin haska mana yanayin ɗabi'un al'umma domin mu gudu tare mu tsira tare. Allah Ya gafarta wa Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi; ya yafe masa kura-kuransa!

**Manazarta**


Ado, A. (2017). *Ra'o'in Bincike Kan Al'adun Hausawa.* Katsina: Kanki Classical Media Enterprises.

Alhassan, H., Musa, U.I. da Zarruƙ, R. M. (1982). *Zaman Hausawa Bugu na Biyu.* Lagos: Islamic Publication Bureau.

Ayuba, A. (2013). "Kyautayin Bahaushe a Waƙoƙin Baka." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sashen Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya.

Bunguɗu, H. U. (2015). "Nazarin Waƙoƙin Bara na Karni na Ashirin da Ɗaya a Zamfara." Kundin Digiri na Uku (Ph.D). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeria, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Bunza, A. M. (2006). *Gadon Feɗe Al'ada.* Lagos: Tiwal Publications Limited.

Bunza, A. M. (2021). "Gudunmawar Kutare ga Adabin Tatsaka Maiwuyar Sani." Maƙalar da Aka Gabatar a Taron Kara wa Juna Sani. Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeria, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Bunza, A. M. (2022). "Tatsaka Maiwuyar Sani (Lalurar Makafta a Al'adance, da Addinance, da Zamanance)." Maƙalar da Aka Gabatar a Taron Kungiyar Makafi Ranar 08 ga Oktoba, 2022 a Jihar Kebbi.

Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya (2006). *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero.* Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Darma, A. Y. (2014). "Farauta a Kasar Katsina." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Ɗalha, I. (2024). "Ba Nakasasshe sai Kasasshe: Nazarin Wasu Al'adun Makafi a Masarautar Katagum." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Ɗanhassan, F. A. (2021)."Rayuwa da Tattalin Arzikin Mata Mabarata a Garin Kaduna."Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Garachi, H. I. (2010). "Nazarin Al'adar Hausawa a Cikin Wasu Nau'o'in Barar Almajirai." Kundin Digiri na Ɗaya (B.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Gusau, S. M. (2003). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Kano: Benchmark Publishers Limited.

Kabakawa, B.U. (2012). "Mahangar Makaɗan Baka Dangane da Tattalin Arziƙin Hausawa." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗnfodiyo.

Magaji, A. (2016). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa.* Ibadan: Spectrum Books Limited.

Musa, A. Y. (2014). "Illar Barace-barace a Ƙasar Hausa: Nazari Kan Wasan Kwaikwayo Mai Taken: Allah Ba Ku Mu Samu." Kundin Digiri na Ɗaya (B.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Sanyinnawal, S. I. (2015). "Jirwayen Sana'o'in Gargajiya a Adabin Bakan Bahaushe." Kundin Digiri na Biyu. Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Sarkin Gulbi, A. (2007). "Nazari Kan Al'adar Bara a Kasar Sakkwato." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Shuni, M. A. (2023). "Nazarin Amfani da Karin Maganganun Hausa na Mutane Masu Bukata ta Musamman." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Sutton, P. W. (2015). *Sociology (7th edition).* United Kingdom: Policy Press.

Umar, H. (2014). "Nazari a Kan Kalmomin Barar Hausawa." Kundin Digiri na Biyu (M.A). Sakkwato: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Yakasai, S. A. (2013). "Dangantakar Harshe da Nakasa." Cikin *Ɗunɗaye Journal of Hausa Studies Vol. 1, No. 6, Pp.116-123.* Sokoto: Department of Nigerisan Languages, Usmanu Danfodiyo University.

Yunusa, A. (2013). "Kuɗi a Idon Makafi: Nazarin Waƙar Kuɗi Ta Malam Haruna Makaho." Cikin *Zauren Waƙa (Journal of Hausa Poetry Sudies). Pp. 274-290.* Sokoto: Department of Nigerian Languages, Usmanu Danfodiyo University.

Yunusa, Y. (1989). *Hausa a Dunƙule.* Kano: Maɗaba'ar Trium, Gidan Sa'adu Zungur.